# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na goma sha ɗaya: Rayuwa a sansanin ’yan gudun hijira


| | |
|---|---|
| Wadda ta rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Jami’in sansani: | ɗan shekara 45 |
| Lami: | ’yar shekara 20 |
| Sa’adatu: | ’yar shekara 35 |
| Charles: | ɗan shekara 45 |
| Matar M. Talle: | ’yar shekara 55 |
| Magaji: | ɗan shekara 22 |
| Ɗan fasa-ƙwauri: | ɗan shekara 45 |

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu”. Wannan shi ne kashi na goma sha ɗaya na wasan kwaikwaiyonmu mai taken “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai”. A cikin shirye-shiryen da suka gabata, kun ji yadda muke bin labarin waɗansu matasa sau da ƙafa, wato: Faisal, da Magaji, da Lami, da kuma yadda suke tinkarar batun ƙaura daga Afirka zuwa Turai.

Sai ku gyara zama domin jin yadda za ta kasance a cikin wannan kashi na yau mai suna “Rayuwa a sansanin ’yan gudun hijira”, inda nan ne aka kai Faisal da sauran ’yan gudun hijirar da suka samu damar tsallakewa zuwa Turai.

**Fitowa ta 1: Faisal a sansanin ’yan gudun hijira a Turai**

**Jami’in sansani:** Kai! Da ku nake. A nan za mu ajiye ku. Idan mun gama bincikenku, za mu ba ku takardun izinin zama na tsawon kwana talatin. Daga nan kuma akwai yiyuwar tasa ƙeyarku zuwa ƙasashenku.

**Faisal:** Wai me wannan yake cewa ne! Gaskiya an samu akasi. Ai da wannan wuri da gidan yari babu wani bambanci. Ga sanyi, ga kuma an kewaye shi da wani shingen waya, ga shi kuma an cinkusa mu mu huɗu a wani ɗan ƙaramin ɗaki.

**Jami’in sansani:** Kai da tunani kake za mu kai ka wani babban otel ne? To, tsaya ka ji, dukkaninku nan kun shigo ne fa ba bisa ƙa’ida ba! Ya kamata ma a ce kun gode wa Allah da kuka samu ma aka killace ku a wani wuri. Za mu ci gaba da ajiye ku a nan har lokacin da za mu gama binciken ƙasar da kowa ya fito. Gara ma kowa ya zauna da shirinsa.

**Faisal:** To, ni abin da nake nema kawai shi ne, a ba ni mafarkar.

Ni daga garin da ake fama da yaƙi na fito, a Gabas ta Tsakiya. Kana ganin kwana nawa ne zai ɗauke ni kafin na samu mafakar?

**Jami’in sansani:** To, wa ya sani. Wataƙila zai kai wata ɗaya, ko biyu, ko uku, ko ma shekara, ko kuma shekara goma. Wai ba dai so kake ka zo Turai ba? To, ai a nan ma Turai take. Daga yanzu za a dinga ba ku karin kumallo kullum da ƙarfe bakwai na safe, abincin rana kuma da ƙarfe ɗaya, na dare kuma da ƙarfe shida da rabi. Idan mutum ya makara, za a yi ba shi. Ka da kowa ya yi tunanin tserewa, muna kallon motsin da kowa yake yi ta cikin kyamarorinmu. Akwai mai wata tambaya? … To madalla. Akwai likitan da zai zo ya duba lafiyarku ɗaya bayan ɗaya. Amma kafin nan, sai kowa ya zauna ya fara tunanin hanyoyin da zai nemi mafarkar, ko kuma ya shafa wa kansa lafiya ya nufi gida kawai. … A rufe wannan ƙofar!

**Faisal:** Gaskiya dai an samu akasi. Ɓa za ta saɓu ba. Ni ban taɓa tsammanin zan samu kaina a haka ba…

**Mai ba da labari:**

A gefe ɗaya kuma ga Lami can ta bar ƙasarta ta haihuwa don ta koma Turai. Taƙaitacciyar ziyarar da ta kawo, da kuma irin alherin da aka ga ta samo, ya sa duk abokai da ƙawayenta suna ɗokin zuwa Turai don su dinga irin rayuwar da take yi. Sai dai kuma shin wace irin rayuwa ce Lamin take yi? Yanzu bari mu bi ta don mu ji irin hirar da suke yi da ƙawarta Sa’adatu da kuma Charles wanda shi ne mutumin da ta aura don ta samu takaradar izinin yin aiki a Turai. Yanzu ga su nan dai a gidan na Charles.

**Fitowa ta 2: Sa'adatu da Lami a gidan Charles**

**Charles:** Kina jina ko Sa'adatu, abin ya ishe ni haka! Ba zan iya ci gaba da wannan harkar ba. Ta faru ta ƙare!

**Sa'adatu:** Haba Charles, mun yi ta nanata wannan magana ba sau ɗaya ba, ba sau biyu ba. Na ce kar ka samu damuwa. Komai zai tafi daidai.

**Charles:** Daga yau babu wani abin da zai sake tafiya daidai. Ai ba kya nan lokacin da suka zo. Duk sai na ji na zama wani soko!

**Lami:** Ka yi haƙuri don Allah! Dawowata a ke nan daga ƙasarmu, kuma ni ba abin da na fahimta. Wai me yake faruwa ne? Akwai wata matsala ne?

**Charles:** Ke ɗin nan, ke ce matsalar. Me ya sa kika bar ƙasar nan?

**Lami:** Tsaya don Allah! Ni na ɗauka cewa wannan auren namu… ni na ɗauka cewa ina da damar na yi duk abin da na ga dama, ko ba haka ba yarjejeniyar tamu take, Sa'a?

**Sa'adatu:** Haka take, Lami. Kin san shi Charles ya damu ne. Lokacin da ba kya nan jami'an shige da fice sun zo nan gidan ba tsammani, suna tambayar dalilin da ya sa kika koma ƙasarku ba tare da mijinki ba.

**Lami:** Allah na gode maka! Daga nan kuma me ya faru? Me suka zo nema? Ko dai sun gane shirin da muka yi ne?

**Charles:** Suna zargin wani abu kam. Sun faɗa cewa sun kama wasu ma'aurata da suka gano cewa auren bogi suka yi don su

taimaka wa baƙi su zauna a Turai don su sami aiki. Don haka yanzu sun buƙace mu mu je mu zauna da su.

**Lami:** Kuma dai? To Sa'adatu, me ya kamata na yi? Kin san fa idan aka mayar da ni ƙasarmu ban san abin da zan yi ba!

**Sa'adatu:** Kai, ku saki jikinku! Ina gaya muku, da ma sun saba yin haka. So suke kawai su razana ku domin su ga ko za ku yi wani kuskure a lokacin da suke yi muku tambayoyi. Kuna jina? Ku tafi kanku tsaye, kar ku karaya. Ke kuma Lami, ki gaya musu cewa wata matasala ce ta gaggawa ta taso a gida, shi ya sa kika tafi.

**Lami:** Ina zuwa. Bari na keɓe na amsa wayar nan.

**Sa'adatu:** Tsaya Lami! Muna fa magana ce a nan mai muhimmanci. Ki tsaya a nan ki amsa wayar mana, kuma ki yi sauri!

**Lami:** Alo? Au Mama ce? Na sauka lafiya, har ma na aiko miki da *text*. Ko ba ki samu ba ne?

**Matar M. Talle:** Kina jina ko Lami? Abin da ya faru...

**Lami:** Mama, me ke faruwa? ƙalau kuke kuwa?

**Matar M. Talle:** Wallahi mota ce ta kaɗe babanki.

**Lami:** Kai! Me kika ce? Haba ba zai yiwu ba! Yaya jikin nasa? Don Allah ki gaya min!

**Matar M. Talle:** Yana can ana kula da shi a asibiti. Kuma likitoci sun ce ba za su iya gaya mana halin da yake ciki ba. … Lami? Kina jina kuwa? Lami?...

**Sa’adatu:** Lafiya kuwa, Lami?

**Charles:** Ta shiga wani hali! Ai faɗuwa ma za ta yi, ta suma. Yi maza ki riƙe ta kafin ta faɗi!

**Mai ba da labari:**
Yanzu dai ta tabbata cewa ƙaryar da Lami ta yi niyyar faɗa wa jami’an shige da fice cewa ta je gida ba tare da mijinta Charles ba saboda wata matsalar gaggawa da ta faru a gida ta zama gaskiya.
Can kuma ga Magaji can yana begen Lami. Ga shi kuma an ƙi yarda a ba shi bizar da ya nema ta shiga Turai a matsayin ɗan yawon buɗe ido saboda an ce ba shi da isasshen kuɗi a cikin banki. Don haka sai yanke shawarar cewa lallai sai ya cika alƙwarin da ya ɗauka ta hanyar bi ta cikin teku don ya kasance da yarinyar da yake ƙauna. Don haka sai ya nemi a ba shi hutu na ’yan kwanaki, ya kuma hau mota ya nufi arewa. Bayan tafiya ta kwanaki, ga shi can ya isa gaɓar tekun Afirka ta Arewa. Kuma ga shi can ya sadu da mutumin nan mai fasa-ƙwaurin mutane wanda ya kai Faisal zuwa Turai. Bari mu ji abin da suke cewa.

**Fitowa ta 3: Magaji ya haɗu da ɗan fasa-ƙwaurin mutane a tashar mota**

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Amma ga alamu ba a nan garin kake ba ko?

**Magaji:** Amm… Gaskiya ne. Wannan shi ne zuwana ƙasar nan na farko.

**Ɗan fasa-ƙwauri:** To, me ya kawo ka? Kai ɗan yawon buɗe ido ne ko kuwa? Ka san fa zuwa nan yana da haɗari, musamman ma yanzu da yake ta fama da tarzoma ga kuma rikicin siyasa.

**Magaji:** Na san da haka. Ni ma akwai irin wannan a ƙasarmu.

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Ah… to, shi ke nan. Ko kana so yin tafiya ne?

**Magaji:** Tafiya? Ban gane ba? Tafiya zuwa ina?

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Zuwa Turai mana.

**Magaji:** Haka ne. Za ka taimaka min ne?

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Kwarai kuwa! Ai ka zo inda ya dace. Kuma ga shi kana da sa'a. Yau ɗin nan wani jirgi ya zo daga Turai, ya kawo wa 'yan gudun hijira kayan agaji. Wani abokina da ke cikin jirgin ya gaya min za a samu wuri idan za su koma. Amma fa wurin mutum ɗaya ne ya rage!

**Magaji:** To, haka ne ko? Yanzu wannan jirgi shi ne zai kai ni zuwa Turai ke nan. In ce dai ba irin ƙananan kwale-kwalen nan naku ba ne?

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Ba ƙaramin kwale-kwale ba ne. Wannan fa babban jirgin ruwa ne. Kuma idan ya ɗauke ku ba inda zai ajiye ku sai a Turai.

**Magaji:** To, nawa zan biya?

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Yuro dubu biyu ne kawai. Ai na yi maka sauƙi. Wannan fa wata dama ce ka samu.

**Magaji:** Yuro dubu biyu! Ai wannan ya fi kuɗin tikitin jirgin sama ma!

**Ɗan fasa-ƙwauri:** Idan haka ne, ka bi jirgin saman mana. Malam, kana ciki

ko ba ka ciki? Saboda ina da abin yi a gabana.

**Magaji:** To shi ke nan, ga kuɗin nan…

**Ɗan fasa-ƙwauri:** A'a, ba a nan za ka ba ni ba. Bari mu keɓe gefe guda. Dawo daga nan! … Yauwa. Ba ni su!

**Mai ba da labari:**

Idan muka juya ga Faisal, za mu ga cewa shi dai ya samu shiga Turai, amma kuma kullum ransa sai daɗa ɓaci yake. Domin kuwa an saka shi a wani ɗan ƙaramin ɗaki mai kama da kurkuku a sansanin 'yan gudun hijira. Ran nan dai bayan da ya gama cin abincin dare, sai ya yanke shawarar dole sai ya ɗauki wani matakin.

**Fitowa ta 4: A sansanin 'yan gudun hijira lokacin cin abincin dare**

**Faisal:** Jama'a, ku saurara don Allah! Ku ɗan saurara! 'Yan'uwana maza da mata! Ina yi muku godiya. Na san wasu daga cikinku ba sa fahimtar abin da nake faɗa tun da ba daga gari ɗaya muka fito ba. To, amma wannan ba wata matsala ba ce, zan ƙoƙarta na ga duk kun fahimce ni. Muhimmin abu dai shi ne yanzu duk ga mu a nan muna fuskantar wahalhalu. Yau fa satinmu guda a nan, amma babu wanda ya zo ya faɗa mana abin da yake faruwa, ko kuma me zai faru a kanmu ba. … Na san cewa mun shigo ƙasar nan ba bisa ƙa'ida ba, amma kuma mu ba masu aikata laifi ba ne. Don me za a cusa mu a cikin keji kamar waɗansu dabbobi, kuma su yi watsi da mu? Mu fa mutane ne, kuma ba abin da muke nema illa zaman lafiya! To, don haka ina ganin ya kamata mu shiga yajin cin abinci. Daga yanzu ba za mu sake cin abinci ba sai dai ruwa, har sai an saurari

matsalolinmu kuma an ba mu mafakar. To, a cikinku su waye suke tare da ni?

**Mai gabatarwa:**

Da wannan tafi da shewa ne da ke fitowa daga wannan sansani na ’yan gudun hijira muka kawo ƙarshen wannan kashi na goma sha ɗaya na shirinmu na “Ji Ka Karu” mai taken “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai”. Idan kuma kuna son ku shiga cikin tattaunawar da ake a kan sansanin ’yan gudun hijira da ke Turai, sai ku bayar da ra’ayoyinku a shafinmu na Facebook, wato facebook.com/dw.lbe. Idan kuma kuna son ku sake sauraron wannan shirin na yau, sai kawai ku tafi shafinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kafin nan, sai mu ce mu jima da yawa.